Duk wanda ya lamunce min abinda ke tsakanin mukamukansa biyu da abinda ke tsakanin kafafuwansa biyu zan lamunce masa aljanna

Daga Sahal Dan Sa'ad - Allah Ya yarda da shi - daga Manzon tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Duk wanda ya lamunce min abinda ke tsakanin mukamukansa biyu da abinda ke tsakanin kafafuwansa biyu zan lamunce masa aljanna".
[Ingantacce ne] [Bukhari ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yana bada labari game da al'amura biyu idan musulmi ya lazimce su to cewa shi zai shiga aljanna, Na farko: Kiyaye harshe daga maganar da zata fusatar da Allah - Madaukakin sarki -. Na biyu: Kiyaye farji daga afkawa a cikin alfasha. Domin cewa wadannan gabubuwa biyun afkawa cikin sabo da su yana yawaita.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/3475